# Surah 018: Kahf -سورة الكهف

بسم الله الرحمن الرحيم

[12:0] Bismi ***ALLAH***, Alrahman, Alrahim.

ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ٱلَّذِىٓ أَنزَلَ عَلَىٰ عَبْدِهِ ٱلْكِتَٰبَ وَلَمْ يَجْعَل لَّهُۥ عِوَجَا ۜ ﴿١﴾

[18:1] Godiya ta tabbata ga ***ALLAH*** wanda ya saukar da littafi a kan bawanSa kuma bai sanya karkata ba a gare shi.

قَيِّمًا لِّيُنذِرَ بَأْسًا شَدِيدًا مِّن لَّدُنْهُ وَيُبَشِّرَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ٱلَّذِينَ
يَعْمَلُونَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أَنَّ لَهُمْ أَجْرًا حَسَنًا ﴿٢﴾

[18:2] Madaidaicin (littafi) domin Ya yi gargadi game da azaba mai radadi daga wurinSa, kuma Ya yi bishara ga muminai wadanda suke aikata ayyuka na qwarai, da cewa suna da lada mai karimci.

مَّٰكِثِينَ فِيهِ أَبَدًا ﴿٣﴾

[18:3] Suna masu zama a cikinta na har abada.

وَيُنذِرَ ٱلَّذِينَ قَالُوا۟ ٱتَّخَذَ ٱللَّهُ وَلَدًا ﴿٤﴾

[18:4] Kuma Ya yi gargadi ga wadanda suka ce, "***ALLAH*** Ya haifi da!"

مَّا لَهُم بِهِۦ مِنْ عِلْمٍ وَلَا لِءَابَآئِهِمْ ۚ كَبُرَتْ كَلِمَةً تَخْرُجُ مِنْ
أَفْوَٰهِهِمْ ۚ إِن يَقُولُونَ إِلَّا كَذِبًا ﴿٥﴾

[18:5] Ba su da wani ilmi game da wannan furcin, kuma iyayensu ba su da shi. Abin da ke fita daga bakinsu yin sabo ne! Abin da suke furtawa babban qarya ne.

فَلَعَلَّكَ بَٰخِعٞ نَّفۡسَكَ عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِمۡ إِن لَّمۡ يُؤۡمِنُواْ بِهَٰذَا ٱلۡحَدِيثِ
أَسَفًا ٦

[18:6] Za ka kusan ka zargi kanka dangane da gurabbansu na wannan hadith, da bijirewa da shi; za ka kusan baqin ciki.

إِنَّا جَعَلۡنَا مَا عَلَى ٱلۡأَرۡضِ زِينَةٗ لَّهَا لِنَبۡلُوَهُمۡ أَيُّهُمۡ أَحۡسَنُ
عَمَلٗا ٧

*Qarshen Duniya*

[18:7] Mun qawaita kome a qasa, domin mu jarrabe su, sa’annan ya bambanta a cikinsu wadanda suke ayyuka na qwarai.

وَإِنَّا لَجَٰعِلُونَ مَا عَلَيۡهَا صَعِيدٗا جُرُزًا ٨

[18:8] Kuma lalle ne, za mu shafe kome da ke kanta, ta rage cikakken bakarare.

أَمۡ حَسِبۡتَ أَنَّ أَصۡحَٰبَ ٱلۡكَهۡفِ وَٱلرَّقِيمِ كَانُواْ مِنۡ ءَايَٰتِنَا
عَجَبًا ٩

[18:9] To, mene ne kuwa ka ke tsamanin abin da yasa muke gaya maka game da as’hab el kahf, da lambobin da ke alaqa da su? Suna cikin mu’ijizanMu na ban mamaki.

**18:8-9 Yadda ya zamanto, tarihin wadannan muminan Kirista, wanda aka sani da sunan ‘As’hab el kahf’ (‘yan bakwai masu barcin kogo) labarin su yana da alaqa kai tsaye da qarshen duniya, wanda aka bayyana a cikin 18:9 da 21. Akwai dalla dallan Manufan wadannan muminai ga bayyana qarshen duniya a shafi na 25.*

إِذۡ أَوَى ٱلۡفِتۡيَةُ إِلَى ٱلۡكَهۡفِ فَقَالُواْ رَبَّنَآ ءَاتِنَا مِن لَّدُنكَ رَحۡمَةٗ وَهَيِّئۡ
لَنَا مِنۡ أَمۡرِنَا رَشَدٗا ١٠

[18:10] Sa’ad da samarin suka yi hijira a cikin ‘kahf’ (kogo), sai suka ce, “Ubangijinmu, ka bamu rahamah daga gare Ka, kuma Ka sa mana albarkacinKa a kan al’amarinmu da shiriyarKa.”

فَضَرَبۡنَا عَلَىٰٓ ءَاذَانِهِمۡ فِي ٱلۡكَهۡفِ سِنِينَ عَدَدٗا ١١

[18:11] Sai muka rufe kunnuwarsu a cikin kogo na qudirin lambobin shekaru.

ثُمَّ بَعَثۡنَٰهُمۡ لِنَعۡلَمَ أَيُّ ٱلۡحِزۡبَيۡنِ أَحۡصَىٰ لِمَا لَبِثُوٓاْ أَمَدٗا ١٢

[18:12] Sa’annan muka tayar da su, domin mu ga kowane dayan gungiyoyin biyu zai iya lissafin adadin lokacin da suka tsaya a wurin.

نَّحۡنُ نَقُصُّ عَلَيۡكَ نَبَأَهُم بِٱلۡحَقِّۚ إِنَّهُمۡ فِتۡيَةٌ ءَامَنُواْ بِرَبِّهِمۡ
وَزِدۡنَٰهُمۡ هُدٗى ١٣

[18:13] Mu ne ke baka wannan labarin, da gaskiya. Lalle ne, su wasu samari ne wanda suka yi imani da Ubangijinsu, kuma muka qara masu shiriya.

وَرَبَطۡنَا عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ إِذۡ قَامُواْ فَقَالُواْ رَبُّنَا رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلۡأَرۡضِ لَن نَّدۡعُوَاْ مِن دُونِهِۦٓ إِلَٰهٗاۖ لَّقَدۡ قُلۡنَآ إِذٗا شَطَطًا ١٤

[18:14] Kuma muka qarfafa masu zukatansu sa’ad da suka yi tsayin daka suka ce: “Ubangijinmu kadai Shi ne Ubangijin sammai da qasa. Ba za mu bautawa wani baicinSa ba. Idan muka yi haka, za mu bata.

هَٰٓؤُلَآءِ قَوْمُنَا ٱتَّخَذُوا۟ مِن دُونِهِۦٓ ءَالِهَةً ۖ لَّوْلَا يَأْتُونَ عَلَيْهِم بِسُلْطَٰنٍۭ بَيِّنٍ ۖ فَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا ﴿١٥﴾

[18:15] Ga mutanenmu suna sanya wasu abin bautawa baicinSa. Idan da ma za su bada wani hujja bayyananna a kan dalilin abin da suke bautawa! To, wane ne mafi zalunci da wanda ya qaga qarya ya dangana su ga ***ALLAH***?

وَإِذِ ٱعْتَزَلْتُمُوهُمْ وَمَا يَعْبُدُونَ إِلَّا ٱللَّهَ فَأْوُۥٓا۟ إِلَى ٱلْكَهْفِ يَنشُرْ لَكُمْ رَبُّكُم مِّن رَّحْمَتِهِۦ وَيُهَيِّئْ لَكُم مِّنْ أَمْرِكُم مِّرْفَقًا ﴿١٦﴾

*As'hab el Kahf Ifsas**

[18:16] "Tun da kuna nufin ku nisance su, su da abin da suke bautawa baicin ***ALLAH***,* bari mu fake a cikin kogo. Ubangijinku Ya sanya maku rahamarSa kuma Ya nuna maku madaidaicin shawerarku."

**18:16-20 Birnin 'Trasus' wurin da Allah Ya sanya samari bakwai, su da karensu, tana kusan mili 200 kudu da tsohon Nisaya, kuma mili 30 kudu da garin Izmiriya cikin qasar Turkiya. Su 'As'hab el Kahf' watau samari bakwai masu barcin kogo, da wadansu samari ne Kiristoci wanda suka so su bi aqidar annabi Isah, domin su bautawa Allah kadai. Sun yi gudun hijira ne domin su guje wa muzgunawar Kiristicin al'adu wanda suka zayyanar da gurbataceyar addini Kirista bayan shekaru dari uku da rasuwar annabi Isah, da bin taron garin Nicene, wurin da aka qago da bayyana tafarkin Uku. A shekara 1928, Franz Miltner, mutumin Austriya masanin ilmin rabon qasa da gine-gine, ya gano kabarin 'yan bakwai masu barkin kogo, watau As'hab el Kahf na Trasus. Labarinsu na qumshe a cikin encyclopedia, watau babban littafi mai taqaita dukkanin fannonin kundin fannoni da dama.*

۞ وَتَرَى ٱلشَّمْسَ إِذَا طَلَعَت تَّزَٰوَرُ عَن كَهْفِهِمْ ذَاتَ ٱلْيَمِينِ وَإِذَا
غَرَبَت تَّقْرِضُهُمْ ذَاتَ ٱلشِّمَالِ وَهُمْ فِى فَجْوَةٍ مِّنْهُ ۚ ذَٰلِكَ مِنْ ءَايَٰتِ
ٱللَّهِ ۗ مَن يَهْدِ ٱللَّهُ فَهُوَ ٱلْمُهْتَدِ ۖ وَمَن يُضْلِلْ فَلَن تَجِدَ لَهُۥ وَلِيًّا
مُّرْشِدًا ﴿١٧﴾

*Majibinci Mai Shiryarwa Shi Ne Farko*

[18:17] Kuma (da kuna wurin) za ku ga rana idan ta fito tana karkata daga kogonsu ta hannun dama, kuma idan ta fadi, tana haska masu daga hagu, da suke ta yin barcinsu a fili. Wannan abu yana daya daga cikin mu'ijizan ALLAH.* Wanda ***ALLAH*** Ya shiriyar shi ne shiriyayyen gaskiya, kuma wanda Ya batar, to, ba za ka samar masa wani majibinci mai shiryarwa ba.

**18:17 Wannan ayah, ko alama, yana gaya mana cewa kogon da tana fuskantar Arewa ne.*

وَتَحْسَبُهُمْ أَيْقَاظًا وَهُمْ رُقُودٌ ۚ وَنُقَلِّبُهُمْ ذَاتَ ٱلْيَمِينِ وَذَاتَ
ٱلشِّمَالِ ۖ وَكَلْبُهُم بَٰسِطٌ ذِرَاعَيْهِ بِٱلْوَصِيدِ ۚ لَوِ ٱطَّلَعْتَ عَلَيْهِمْ
لَوَلَّيْتَ مِنْهُمْ فِرَارًا وَلَمُلِئْتَ مِنْهُمْ رُعْبًا ﴿١٨﴾

[18:18] Kuma (da kun kasance wurin) za ku zaton su farkakku ne, alhali kuwa su masu barci ne. muna juya su zuwa dama da ta hagu, kuma karensu yana miqan qafafuwansa a tsakaninsu. Da kun kallesu, da za ku sheqa a guje daga gare su, saboda tsoro.

وَكَذَٰلِكَ بَعَثْنَٰهُمْ لِيَتَسَآءَلُوا۟ بَيْنَهُمْ ۚ قَالَ قَآئِلٌ مِّنْهُمْ كَمْ
لَبِثْتُمْ ۖ قَالُوا۟ لَبِثْنَا يَوْمًا أَوْ بَعْضَ يَوْمٍ ۚ قَالُوا۟ رَبُّكُمْ أَعْلَمُ بِمَا لَبِثْتُمْ
فَٱبْعَثُوٓا۟ أَحَدَكُم بِوَرِقِكُمْ هَٰذِهِۦٓ إِلَى ٱلْمَدِينَةِ فَلْيَنظُرْ أَيُّهَآ
أَزْكَىٰ طَعَامًا فَلْيَأْتِكُم بِرِزْقٍ مِّنْهُ وَلْيَتَلَطَّفْ وَلَا يُشْعِرَنَّ
بِكُمْ أَحَدًا ١٩

[18:19] Kuma ta haka ne muka tayar da su, domin su tambayi junansu, “Wani mai magana daga cikinsu ya ce, “Tun yaushe ne kuke nan?” Suka ce, “Muna nan na yini daya ko sahen yini,” suka amsa. “Ubangijinku ne mafi sani ga tun yaushe muke nan, to, bari mu aiki dayanku da wannan azurfarku zuwa cikin gari. Bari ya je ya nemo mana mafi tsakin abin dafawa, ya saya mana. Amma sai ya yi a hankali, kada ya ja hankali game da ku ga wani.

إِنَّهُمْ إِن يَظْهَرُوا۟ عَلَيْكُمْ يَرْجُمُوكُمْ أَوْ يُعِيدُوكُمْ فِى مِلَّتِهِمْ
وَلَن تُفْلِحُوٓا۟ إِذًا أَبَدًا ٢٠

[18:20] “Idan suka kama ku, za su jefe ku, ko kuwa su tilasta ku, domin ku koma zuwa addininsu, sa’annan ba za ku ci nasara ba.”

وَكَذَٰلِكَ أَعْثَرْنَا عَلَيْهِمْ لِيَعْلَمُوٓا۟ أَنَّ وَعْدَ ٱللَّهِ حَقٌّ وَأَنَّ ٱلسَّاعَةَ
لَا رَيْبَ فِيهَآ إِذْ يَتَنَٰزَعُونَ بَيْنَهُمْ أَمْرَهُمْ ۖ فَقَالُوا۟ ٱبْنُوا۟ عَلَيْهِم بُنْيَٰنًا ۖ
رَّبُّهُمْ أَعْلَمُ بِهِمْ ۚ قَالَ ٱلَّذِينَ غَلَبُوا۟ عَلَىٰٓ أَمْرِهِمْ لَنَتَّخِذَنَّ عَلَيْهِم
مَّسْجِدًا ﴿٢١﴾

*Alaqa Da Qarshen Duniya**

[18:21] Sai muka yi sanadin a gano su, domin mu bari kowa ya san cewa wa’adin ***ALLAH*** gaskiya ne, kuma mu cire shakka game da qarshen duniya.* Sa’annan mutane suka yi jayayya a tsakanin junansu game da su. Wadansu suka ce, “Bari mu yi gini a wurinsu.” Ubangijinsu ne mafi sani game da su. Wadanda suka rinjaya suka ce, “Za mu gina masallaci wurinsu.”

**18:21 Kamar yadda dalla dallan bayani yake a cikin shafi 25, wannan tarihin ya taimaka wurin gano bakin alura dangane da qarshen duniya.*

سَيَقُولُونَ ثَلَٰثَةٌ رَّابِعُهُمْ كَلْبُهُمْ وَيَقُولُونَ خَمْسَةٌ سَادِسُهُمْ
كَلْبُهُمْ رَجْمًۢا بِٱلْغَيْبِ ۖ وَيَقُولُونَ سَبْعَةٌ وَثَامِنُهُمْ كَلْبُهُمْ ۚ قُل رَّبِّىٓ
أَعْلَمُ بِعِدَّتِهِم مَّا يَعْلَمُهُمْ إِلَّا قَلِيلٌ ۗ فَلَا تُمَارِ فِيهِمْ إِلَّا مِرَآءً ظَٰهِرًا وَلَا
تَسْتَفْتِ فِيهِم مِّنْهُمْ أَحَدًا ﴿٢٢﴾

[18:22] Wadansu za su ce, “Da su uku ne; karensu ne na hudunsu,” alhali kuwa wasu za su ce su, “Biyar ne; karensu ne na shida,” da suke ta cinci. Wadansu suna cewa, “Bakwai ne, da na takwas dinsu karensu. Ka ce, “Ubangijina ne mafi sani adadin lambarsu.” Kadan ne kawai suka san adadin

lambarsu daidai. Saboda haka, kada ka yi jayayya da su; ku yarda da su kawai. Kuma kada ka yi fatawa ga kowa game da wannan.

وَلَا تَقُولَنَّ لِشَاْىْءٍ إِنِّى فَاعِلٌ ذَٰلِكَ غَدًا ﴿٢٣﴾

*Ambatar Allah*

*A Kowane Daman Da Muka Samu*

[18:23] Kada ka ce za ka aikata wani abu nan gaba,

إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ ۚ وَٱذْكُر رَّبَّكَ إِذَا نَسِيتَ وَقُلْ عَسَىٰٓ أَن يَهْدِيَنِ
رَبِّى لِأَقْرَبَ مِنْ هَٰذَا رَشَدًا ﴿٢٤﴾

[18:24] ba tare da ka ce, “Insha ***ALLAH***.” Idan ka manta baka ce hakan ba, sai ka tuna Ubangijinka nan da nan kuma ka ce, “Ubangijina Ya shiriyar da ni domin in gyara wani sa’a.”

**18:24 Wannan muhimmiyar umurni ce da ke bamu daman tunawa da Allah ala kullu yaumin.*

وَلَبِثُوا۟ فِى كَهْفِهِمْ ثَلَٰثَ مِا۟ئَةٍ سِنِينَ وَٱزْدَادُوا۟ تِسْعًا ﴿٢٥﴾

[18:25] Sun tsaya a cikin kogonsu shekaru dari uku, aka qara da tara.*

**18:25 Bambancin shekaru 300 qidayan watan rana, da shekaru 300 na watan muhammadiya, shekaru tara ne. ta haka ne, madaukakin sarki Ya qaddara gano qarshen duniya ya faru a cikin AD 1980 (1400 AH), shekaru 300 (309 shekarun watan muhamamdiya) gabanin qarshen duniya (dubi 72:27 da shafi 25).*

قُلِ ٱللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا لَبِثُوا۟ ۖ لَهُۥ غَيْبُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ أَبْصِرْ بِهِۦ
وَأَسْمِعْ ۚ مَا لَهُم مِّن دُونِهِۦ مِن وَلِىٍّ وَلَا يُشْرِكُ فِى حُكْمِهِۦٓ
أَحَدًا ٢٦

[18:26] Ka ce, "***ALLAH*** ne mafi sanin adadin lokutan da suka tsaya a wurin." Shi ne da sanin gaibun sammai da qasa. Da izininSa za ka iya gani; da izininSa za ka iya ji. Babu wani majibinci baicinSa, kuma ba Ya tarayya da kowa a cikin hukuncinSa.

وَٱتْلُ مَآ أُوحِىَ إِلَيْكَ مِن كِتَابِ رَبِّكَ ۖ لَا مُبَدِّلَ لِكَلِمَٰتِهِۦ وَلَن
تَجِدَ مِن دُونِهِۦ مُلْتَحَدًا ٢٧

[18:27] Ka karanta abin da aka yi wahayi zuwa gare ka na littafin Ubangijinka. Babu wani abu mai kau da kalmominSa, kuma ba za ka sami wata madogara ba baicin shi.

وَٱصْبِرْ نَفْسَكَ مَعَ ٱلَّذِينَ يَدْعُونَ رَبَّهُم بِٱلْغَدَوٰةِ وَٱلْعَشِىِّ
يُرِيدُونَ وَجْهَهُۥ ۖ وَلَا تَعْدُ عَيْنَاكَ عَنْهُمْ تُرِيدُ زِينَةَ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ۖ
وَلَا تُطِعْ مَنْ أَغْفَلْنَا قَلْبَهُۥ عَن ذِكْرِنَا وَٱتَّبَعَ هَوَىٰهُ وَكَانَ أَمْرُهُۥ
فُرُطًا ٢٨

*Karatun Alqurani Tare*

[18:28] Ka yi haqurin tilasta kanka da zama tare da wadanda ke kiran Ubangijinsu safe da maraice, suna neman yardanSa. Kuma kada idanunka su juya ga barinsu, kana neman wuqiniyan rayuwar duniya. Kumar kada ka

bi wanda muka shagaltar da zuciyarsa daga hukuncinMu; wanda yake bin son zuciyarsa, kuma wanda ya rikitad da al’amarinsa.

وَقُلِ ٱلْحَقُّ مِن رَّبِّكُمْ ۖ فَمَن شَآءَ فَلْيُؤْمِن وَمَن شَآءَ فَلْيَكْفُرْ ۚ إِنَّآ
أَعْتَدْنَا لِلظَّٰلِمِينَ نَارًا أَحَاطَ بِهِمْ سُرَادِقُهَا ۚ وَإِن يَسْتَغِيثُوا۟ يُغَاثُوا۟
بِمَآءٍ كَٱلْمُهْلِ يَشْوِى ٱلْوُجُوهَ ۚ بِئْسَ ٱلشَّرَابُ وَسَآءَتْ
مُرْتَفَقًا ﴿٢٩﴾

*Cikakken ‘Yanci Ga Addini*

[18:29] Ka zayyana: “Wannan shi ne gaskiya daga Ubangijinku,” saboda haka wanda ya so, to, ya yi imani, kuma wanda ya so, to, ya kafirta. Mun shirya wa azzalumai wuta, wanda shamakunta zai kewaye su. Idan suka yi kukan neman taimako, za ba su wani abu na ruwa-ruwa, kamar dabzar mai na acid mai qona fuskoki. Tir da abin shansu na zullumi! Kuma tir da makoman zullumi!

إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ إِنَّا لَا نُضِيعُ أَجْرَ مَنْ
أَحْسَنَ عَمَلًا ﴿٣٠﴾

[18:30] Amma ga wadanda suka yi imani kuma suka aikata ayyuka na qwarai, ba rasa baiwa lada ga wadanda suka kyautata ayyukan qwarai.

أُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمْ جَنَّٰتُ عَدْنٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهِمُ ٱلْأَنْهَٰرُ يُحَلَّوْنَ فِيهَا مِنْ
أَسَاوِرَ مِن ذَهَبٍ وَيَلْبَسُونَ ثِيَابًا خُضْرًا مِّن سُندُسٍ وَإِسْتَبْرَقٍ مُّتَّكِـِٔينَ
فِيهَا عَلَى ٱلْأَرَآئِكِ ۚ نِعْمَ ٱلثَّوَابُ وَحَسُنَتْ مُرْتَفَقًا ﴿٣١﴾

[18:31] Wadannan sun cancanci gidajen Aljannah wurin da qoramu suke gudana daga qarqashinsu. Za qawaita masu a wurin da suluwan zinariya, kuma za su sa tufafin siliki da karammiski masu ruwan kore, kuma za su huta a kan karagu suna holewa. Sambarika da sakamakonsu; kuma sambarika da qasaitacen wurin mahuta!

۞ وَاضْرِبْ لَهُم مَّثَلًا رَّجُلَيْنِ جَعَلْنَا لِأَحَدِهِمَا جَنَّتَيْنِ مِنْ أَعْنَابٍ
وَحَفَفْنَاهُمَا بِنَخْلٍ وَجَعَلْنَا بَيْنَهُمَا زَرْعًا ﴿٣٢﴾

*Muhalli A Matsayin Abin Shirka*

[18:32] Kuma ka buga masu misali da wasu mutane biyu: mun baiwa dayansu gonaki biyu na inabobi, kuma muka kewaye su da itacen dabinai, kuma muka sanya wasu shuke-shuke a tsakanin gonakin.

**18:32-42 Alqurani ya buga misalai da dama na abubuwan shirka dabam dabam wanda mutane suke bauta baicin Allah; wanda suka hada da yara [7:190], shugabanin addinai da shehunai [9:31], muhalli [18:42], matattun waliyai da annabawa [16:20-21, 35:14, da 46:5-6], da kuma son kai [25:43, 45:23].*

كِلْتَا الْجَنَّتَيْنِ آتَتْ أُكُلَهَا وَلَمْ تَظْلِم مِّنْهُ شَيْئًا ۚ وَفَجَّرْنَا خِلَالَهُمَا
نَهَرًا ﴿٣٣﴾

[18:33] Kowace gona daga biyun, ta bayar da amfaninta a cikin lokaci, da kariminci, saboda mun sanya qorami ta gudana a tsakaninsu.

وَكَانَ لَهُ ثَمَرٌ فَقَالَ لِصَاحِبِهِ وَهُوَ يُحَاوِرُهُ أَنَا أَكْثَرُ مِنكَ مَالًا وَأَعَزُّ
نَفَرًا ﴿٣٤﴾

[18:34] Wata rana, bayan girbi, ya yi alfaharin gayawa abokinsa cewa: “Ni ne mafificin wadata a kanka, kuma ni ne mafi mutunci daga wurin mutane.”

وَدَخَلَ جَنَّتَهُۥ وَهُوَ ظَالِمٌ لِّنَفْسِهِۦ قَالَ مَآ أَظُنُّ أَن تَبِيدَ هَٰذِهِۦٓ
أَبَدًا ﴿٣٥﴾

[18:35] Kuma sa’ad da ya shiga gonansa, sai ya zalunci kansa da cewa, “Ba ni zaton wannan zai taba qarewa ba.

وَمَآ أَظُنُّ ٱلسَّاعَةَ قَآئِمَةً وَلَئِن رُّدِدتُّ إِلَىٰ رَبِّى لَأَجِدَنَّ خَيْرًا
مِّنْهَا مُنقَلَبًا ﴿٣٦﴾

[18:36] Kumar ba ni zaton sa’a (Alqiyamah) mai tsayuwa ce. Kuma ko da an mayar da ni ne ga Ubangijina, zan ( koma samun dabara) in mallaki abin da ya dara wannan a can.”

قَالَ لَهُۥ صَاحِبُهُۥ وَهُوَ يُحَاوِرُهُۥٓ أَكَفَرْتَ بِٱلَّذِى خَلَقَكَ مِن تُرَابٍ ثُمَّ مِن
نُّطْفَةٍ ثُمَّ سَوَّىٰكَ رَجُلًا ﴿٣٧﴾

[18:37] Abokinsa ya ce masa, sa’ad da yake muhawara da shi, “Shin ka kafirta ne ga wanda Ya halitta ka daga turbaya, sa’annan daga digon maniyi, sa’annan Ya daidaita ka, ka zama mutum?

لَّٰكِنَّا۠ هُوَ ٱللَّهُ رَبِّى وَلَآ أُشْرِكُ بِرَبِّىٓ أَحَدًا ﴿٣٨﴾

[18:38] “Ni kam, ***ALLAH*** ne Ubangijina, kuma ba zan yi shirka da kowane abu ba da Ubangijina.

وَلَوْلَآ إِذْ دَخَلْتَ جَنَّتَكَ قُلْتَ مَا شَآءَ ٱللَّهُ لَا قُوَّةَ إِلَّا بِٱللَّهِ ۚ إِن تَرَنِ
أَنَا۠ أَقَلَّ مِنكَ مَالًا وَوَلَدًا ﴿٣٩﴾

*Muhimmin Umurni*

[18:39] "Sa'ad da ka shiga gonarka, da ya kamata ka ce, Ma Sha ***ALLAH***. La Quwwata Illa Bi'***ALLAH***. Za ka ga cewa ni ba ni da dukiya da yara kamar ka.

فَعَسَىٰ رَبِّىٓ أَن يُؤْتِيَنِ خَيْرًا مِّن جَنَّتِكَ وَيُرْسِلَ عَلَيْهَا حُسْبَانًا
مِّنَ ٱلسَّمَآءِ فَتُصْبِحَ صَعِيدًا زَلَقًا ﴿٤٠﴾

[18:40] To, amma Ubangijina zai iya ya bani gona fiye da naka. Kuma zai iya ya aika da goguwar iskan hadari daga sama wanda za ta shafe gonarka, ta bar shi bakarare.

أَوْ يُصْبِحَ مَآؤُهَا غَوْرًا فَلَن تَسْتَطِيعَ لَهُۥ طَلَبًا ﴿٤١﴾

[18:41] "Ko kuma, ruwanta ta nutsad da zurufi, inda ba za ka iya kaiwa ba."

وَأُحِيطَ بِثَمَرِهِۦ فَأَصْبَحَ يُقَلِّبُ كَفَّيْهِ عَلَىٰ مَآ أَنفَقَ فِيهَا وَهِىَ خَاوِيَةٌ عَلَىٰ
عُرُوشِهَا وَيَقُولُ يَٰلَيْتَنِى لَمْ أُشْرِكْ بِرَبِّىٓ أَحَدًا ﴿٤٢﴾

[18:42] Kuma haka ne, an shafe gonarsa, sai ya yai gari yana nadama, yana koke saboda abin da ya kashe a banza a cikinta, sa'ad da aka bari gonansa bakarare. Daga qarshe sai ya ce, "Kaitona, da ma ban yi shirkanta gona na da Ubangijina ba."

وَلَمْ تَكُن لَّهُۥ فِئَةٌ يَنصُرُونَهُۥ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَمَا كَانَ مُنتَصِرًا ﴿٤٣﴾

[18:43] kuma da babu wani mai tallafa masa ga ***ALLAH***, kuma ba wanda ya iya ya basi wani taimako.

هُنَالِكَ ٱلْوَلَٰيَةُ لِلَّهِ ٱلْحَقِّ ۚ هُوَ خَيْرٌ ثَوَابًا وَخَيْرٌ عُقْبًا ﴿٤٤﴾

[18:44] Dalili shi ne taimakon gaskiya da jibinta daga ***ALLAH*** yake; Yana ba da mafificin lada, kuma da mafificin aqiba.

وَٱضْرِبْ لَهُم مَّثَلَ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا كَمَآءٍ أَنزَلْنَٰهُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ فَٱخْتَلَطَ بِهِۦ نَبَاتُ ٱلْأَرْضِ فَأَصْبَحَ هَشِيمًا تَذْرُوهُ ٱلرِّيَٰحُ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ مُّقْتَدِرًا ﴿٤٥﴾

[18:45] Ka buga masu misalin rayuwar duniya, kamar ruwa ne wanda muka sakar daga sama domin ya fito da tsiro a qasa, sa'annan suka koma baro wanda tafi da hurin iska. Kuma ***ALLAH*** Ya kasance mai yawan ikon yi a kan dukan kome.

ٱلْمَالُ وَٱلْبَنُونَ زِينَةُ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ۖ وَٱلْبَٰقِيَٰتُ ٱلصَّٰلِحَٰتُ خَيْرٌ عِندَ رَبِّكَ ثَوَابًا وَخَيْرٌ أَمَلًا ﴿٤٦﴾

*Yin Gyara Ga Al'amrarmu*

[18:46] Kudi da yara su ne qawar rayuwar duniya, amma ayyuka na qwarai sun fi zama alheri daga Ubangijinka ga lada, kuma mafi alheri ga buri.

وَيَوْمَ نُسَيِّرُ ٱلْجِبَالَ وَتَرَى ٱلْأَرْضَ بَارِزَةً وَحَشَرْنَٰهُمْ فَلَمْ نُغَادِرْ مِنْهُمْ أَحَدًا ﴿٤٧﴾

[18:47] Akwai ranar da za mu shafe tsaunika, kuma za ku ga qasa bakarareya. Sa,annan mu tara su duka, ba za mu bar ko dayansu ba.

وَعُرِضُوا۟ عَلَىٰ رَبِّكَ صَفًّا لَّقَدْ جِئْتُمُونَا كَمَا خَلَقْنَٰكُمْ أَوَّلَ مَرَّةٍۭ ۚ بَلْ
زَعَمْتُمْ أَلَّن نَّجْعَلَ لَكُم مَّوْعِدًا ﴿٤٨﴾

[18:48] Za gufanad da su a gaban Ubangijinka a cikin sahu guda. Kun zo mana yasu-yasunku, kamar yadda muka halicce ku farkon lokaci. Lalle ne, da abin da kuka riya cewan ba zai taba faruwa ba kenan.

وَوُضِعَ ٱلْكِتَٰبُ فَتَرَى ٱلْمُجْرِمِينَ مُشْفِقِينَ مِمَّا فِيهِ وَيَقُولُونَ
يَٰوَيْلَتَنَا مَالِ هَٰذَا ٱلْكِتَٰبِ لَا يُغَادِرُ صَغِيرَةً وَلَا كَبِيرَةً إِلَّآ
أَحْصَىٰهَا ۚ وَوَجَدُوا۟ مَا عَمِلُوا۟ حَاضِرًا ۗ وَلَا يَظْلِمُ رَبُّكَ أَحَدًا ﴿٤٩﴾

[18:49] Za gabatar da littafin ayyuka, kuma za ka ga mai laifi yana fargaban abin da ya qumsa. Za su ce, “Kaitonmu. Yahya aka yi wannan littafin bai bar kome ba, qarami ko babba, ba tare da ya qidaya shi ba?” Za su tarad da kome da suka aikata an gabatar da shi. Ubangijinka ba ya zaluntar kowa.

وَإِذْ قُلْنَا لِلْمَلَٰٓئِكَةِ ٱسْجُدُوا۟ لِءَادَمَ فَسَجَدُوٓا۟ إِلَّآ إِبْلِيسَ كَانَ مِنَ ٱلْجِنِّ
فَفَسَقَ عَنْ أَمْرِ رَبِّهِۦٓ ۗ أَفَتَتَّخِذُونَهُۥ وَذُرِّيَّتَهُۥٓ أَوْلِيَآءَ مِن دُونِى وَهُمْ
لَكُمْ عَدُوٌّۢ ۚ بِئْسَ لِلظَّٰلِمِينَ بَدَلًا ﴿٥٠﴾

*Nau’in Halittan Allah*

[18:50] Sa’ad da muka ce wa mala’iku, “Ku yi sujadah ga Adam.” Sai suka yi sujadah, ban da Iblis. Sai ya kasance aljanni, saboda ya finjire bin umurnin Ubangijinsa.* To, shin, za ku zabe shi, shi da zuriyarsa a matsayin majibinta baicin Ni, duk da cewan su maqiyanku ne? Wannan shi ne musaya da azzalumai na zullumi!

**18:50 A lokacin da aka yi tarna mai girma a cikin duniyar sama [38:69], an yi nau'in dukan halittu cikin mala'iku, aljannu da mutane (shafi ta 7).*

۞ مَّآ أَشْهَدتُّهُمْ خَلْقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَلَا خَلْقَ أَنفُسِهِمْ وَمَا
كُنتُ مُتَّخِذَ ٱلْمُضِلِّينَ عَضُدًا ﴿٥١﴾

[18:51] Ban bari su shaida game da halittar sammai da qasa ba, ko kuma halittar kansu. Kuma bana bari mugu ya yi aiki a cikin masarautaNa.

**18:51 Allah ne mafi sani Iblis da masu taya shi aiki, watau aljannu da mutane, cewa za su yanke shawarin da bai dace ba. Dalili kenan da ya sa aka kange su daga shaidan dabarun halitta.*

وَيَوْمَ يَقُولُ نَادُوا۟ شُرَكَآءِىَ ٱلَّذِينَ زَعَمْتُمْ فَدَعَوْهُمْ فَلَمْ يَسْتَجِيبُوا۟
لَهُمْ وَجَعَلْنَا بَيْنَهُم مَّوْبِقًا ﴿٥٢﴾

[18:52] Akwai ranar da zai ce, "Ku kira abokan tarayyaTa, wanda kuke riya su ne baicin Ni," za su kira su, amma ba za su amsa masu ba. Shamakin ***'maubiqa'*** zai rabe su daga junansu.

وَرَءَا ٱلْمُجْرِمُونَ ٱلنَّارَ فَظَنُّوٓا۟ أَنَّهُم مُّوَاقِعُوهَا وَلَمْ يَجِدُوا۟ عَنْهَا
مَصْرِفًا ﴿٥٣﴾

[18:53] Masu laifi za su ga wuta, kuma za su tabbatar cewa za su fada ne a cikinta. Ba za su sami kubucewa ba daga gare ta.

وَلَقَدْ صَرَّفْنَا فِى هَٰذَا ٱلْقُرْءَانِ لِلنَّاسِ مِن كُلِّ مَثَلٍ ۚ وَكَانَ ٱلْإِنسَٰنُ
أَكْثَرَ شَىْءٍ جَدَلًا ﴿٥٤﴾

*Kafirai Sun Qi Su Amince*

*Da Cikan Alqurani*

[18:54] Mun bada kowane irin misali a cikin wannan Alqurani ga mutane, amma mutum ya kasance halitta mafi yawan jayayya.

وَمَا مَنَعَ ٱلنَّاسَ أَن يُؤْمِنُوٓا۟ إِذْ جَآءَهُمُ ٱلْهُدَىٰ وَيَسْتَغْفِرُوا۟ رَبَّهُمْ
إِلَّآ أَن تَأْتِيَهُمْ سُنَّةُ ٱلْأَوَّلِينَ أَوْ يَأْتِيَهُمُ ٱلْعَذَابُ قُبُلًا ٥٥

[18:55] Babu abin da ya hana mutum daga yin imani, sa’ad da shiriya ya je masu, kuma daga neman gafara daga Ubangijinsu, sai dai cewa sun nemi su ga (irin mu’ijizai) kamar na mutanen da, ko kuwa su ga azaba tukuna.

وَمَا نُرْسِلُ ٱلْمُرْسَلِينَ إِلَّا مُبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ ۚ وَيُجَٰدِلُ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ بِٱلْبَٰطِلِ لِيُدْحِضُوا۟ بِهِ ٱلْحَقَّ ۖ وَٱتَّخَذُوٓا۟ ءَايَٰتِى وَمَآ أُنذِرُوا۟
هُزُوًا ٥٦

18:56] Mu kan aika da manzanni ne kawai domin su ba da bushara, kuma da gargadi. Wadanda suka kafirta suna jayayya da qarya daomin su kayar da gaskiya, kuma suna daukan ayoyiNa da gargadiNa a banza.

وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن ذُكِّرَ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِۦ فَأَعْرَضَ عَنْهَا وَنَسِىَ مَا قَدَّمَتْ يَدَاهُ ۚ إِنَّا
جَعَلْنَا عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ أَكِنَّةً أَن يَفْقَهُوهُ وَفِىٓ ءَاذَانِهِمْ وَقْرًا ۖ وَإِن
تَدْعُهُمْ إِلَى ٱلْهُدَىٰ فَلَن يَهْتَدُوٓا۟ إِذًا أَبَدًا ٥٧

*Aikin Matsakancin Ikon Alllah*

[18:57] Wane ne mafi zalunci da wanda aka tunatar game da ayoyin Ubangijinsa, sai ya bijire da barinsu, ba tare da sanin abin da suke yi ba. Saboda haka, muka sanya abubuwan rufi a kan zukatansu domin kada su

fahimce shi (Alqur'ani), kuma a cikin kunnuwansu. Ta haka ne, duk kome da za ka yi, ka shiriyad da su, ba za su shiryu ba, har abada.

وَرَبُّكَ ٱلْغَفُورُ ذُو ٱلرَّحْمَةِ ۖ لَوْ يُؤَاخِذُهُم بِمَا كَسَبُوا۟ لَعَجَّلَ لَهُمُ
ٱلْعَذَابَ ۚ بَل لَّهُم مَّوْعِدٌ لَّن يَجِدُوا۟ مِن دُونِهِۦ مَوْئِلًا ﴿٥٨﴾

[18:58] Duk da haka, Ubangijinka mai gafara ne, mai yawan rahamah. Idan da zai kama su saboda abin da suka aikata, da ya shafe su nan da nan. Amma a maimakon haka, sai Ya jinkirta masu sai qayyadadden lokaci, sa'an da aka qaddarta; sa'annan ba za su kubuta ba.

وَتِلْكَ ٱلْقُرَىٰٓ أَهْلَكْنَٰهُمْ لَمَّا ظَلَمُوا۟ وَجَعَلْنَا لِمَهْلِكِهِم
مَّوْعِدًا ﴿٥٩﴾

[18:59] Alqaryu masu yawa wanda muka halaka saboda zaluncinsu, sai da muka sanya qayyadadden lokaci na halaka su.

وَإِذْ قَالَ مُوسَىٰ لِفَتَىٰهُ لَآ أَبْرَحُ حَتَّىٰٓ أَبْلُغَ مَجْمَعَ
ٱلْبَحْرَيْنِ أَوْ أَمْضِىَ حُقُبًا ﴿٦٠﴾

*Darussa Masu Amfani Daga Musa Da Malaminsa*

[18:60] A lokacin da Musa ya ce wa bawansa, "Ba zan huta ba sai na isa wurin da rafi biyu suka game, kome nisan shi."

فَلَمَّا بَلَغَا مَجْمَعَ بَيْنِهِمَا نَسِيَا حُوتَهُمَا فَٱتَّخَذَ سَبِيلَهُۥ فِى ٱلْبَحْرِ
سَرَبًا ﴿٦١﴾

[18:61] A lokacin da suka kai dam da wurin da magamar tsakaninsu, sai suka manta da kifinsu, sai ta kama hanyan komawa zuwa rafi, a labe.

فَلَمَّا جَاوَزَا قَالَ لِفَتَىٰهُ ءَاتِنَا غَدَآءَنَا لَقَدْ لَقِينَا مِن سَفَرِنَا هَٰذَا
نَصَبًا ﴿٦٢﴾

18:62] A lokacin da suka wuce wurin, sai ya ce wa bawansa, “Ka kawo mana kalacinmu. Tafiyar nan ta gajiyar da mu matuqa.”

قَالَ أَرَءَيْتَ إِذْ أَوَيْنَآ إِلَى ٱلصَّخْرَةِ فَإِنِّى نَسِيتُ ٱلْحُوتَ وَمَآ أَنسَىٰنِيهُ إِلَّا
ٱلشَّيْطَٰنُ أَنْ أَذْكُرَهُۥ ۚ وَٱتَّخَذَ سَبِيلَهُۥ فِى ٱلْبَحْرِ عَجَبًا ﴿٦٣﴾

[18:63] Ya ce, “Ka tuna sa’ad da muka zauna kusa da wani dutse bayan can? Ban ba da hankali ga kifin ba. Iblis ne ya sa na manta da ita, sai ta kama hanyanta komawa zuwa ruwa, ta garibi.”

قَالَ ذَٰلِكَ مَا كُنَّا نَبْغِ ۚ فَٱرْتَدَّا عَلَىٰٓ ءَاثَارِهِمَا قَصَصًا ﴿٦٤﴾

[18:64] (Musa) ya ce, “To, daidan wurin da muke nema kenan.” Sai suka koma bin sawun qafansu baya.

فَوَجَدَا عَبْدًا مِّنْ عِبَادِنَآ ءَاتَيْنَٰهُ رَحْمَةً مِّنْ عِندِنَا وَعَلَّمْنَٰهُ مِن
لَّدُنَّا عِلْمًا ﴿٦٥﴾

[18:65] Sai suka sami daya daga bayinMu, wanda muka bashi wata rahamah daga wurinMu, kuma muka koya masa wani ilmi daga wurinMu.

قَالَ لَهُۥ مُوسَىٰ هَلْ أَتَّبِعُكَ عَلَىٰٓ أَن تُعَلِّمَنِ مِمَّا عُلِّمْتَ رُشْدًا ﴿٦٦﴾

[18:66] Musa ya ce masa, “Ko in bi ka, domin ka koya mani daga abin da aka koya maka na shiriya?”

قَالَ إِنَّكَ لَن تَسْتَطِيعَ مَعِيَ صَبْرًا ﴿٦٧﴾

[18:67] Ya ce, "Ba za ka iya yin juriya tare da ni ba."

وَكَيْفَ تَصْبِرُ عَلَىٰ مَا لَمْ تُحِطْ بِهِۦ خُبْرًا ﴿٦٨﴾

[18:68] Ta yaya za ka iya juriya ga abin da baka sani ba?"

قَالَ سَتَجِدُنِيٓ إِن شَآءَ ٱللَّهُ صَابِرًا وَلَآ أَعْصِي لَكَ أَمْرًا ﴿٦٩﴾

[18:69] Ya ce, "Insha ALLAH, za ka ga cewa ni mai haquri ne. Ba zan qi bin umurnin da ka yi mani ba."

قَالَ فَإِنِ ٱتَّبَعْتَنِي فَلَا تَسْـَٔلْنِي عَن شَيْءٍ حَتَّىٰٓ أُحْدِثَ لَكَ مِنْهُ
ذِكْرًا ﴿٧٠﴾

[18:70] Ya ce, "Idan ka bi ni, to, kada ka tambaye ni game da kome, sai idan na ga daman in gaya maka game da shi."

فَٱنطَلَقَا حَتَّىٰٓ إِذَا رَكِبَا فِي ٱلسَّفِينَةِ خَرَقَهَا ۖ قَالَ أَخَرَقْتَهَا لِتُغْرِقَ أَهْلَهَا
لَقَدْ جِئْتَ شَيْـًٔا إِمْرًا ﴿٧١﴾

[18:71] Sai suka tafi. A lokacin da suka hau cikin girgi, sai ya huda ta. Ya ce, "Ka huda ta ne domin ta nutsar da mutanenta? Lalle, ka aikata mumunan abu."

قَالَ أَلَمْ أَقُلْ إِنَّكَ لَن تَسْتَطِيعَ مَعِيَ صَبْرًا ﴿٧٢﴾

[18:72] Ya ce, "Ashe, ban ce ba za ka iya juriya tare da ni ba?"

قَالَ لَا تُؤَاخِذْنِي بِمَا نَسِيتُ وَلَا تُرْهِقْنِي مِنْ أَمْرِي عُسْرًا ﴿٧٣﴾

[18:73] Ya ce, "Ka yi haquri. Kada ka hukunta ni bisa ga mantuwana; kuma kada ka kallafa mini tsanani ga al'amarina."

فَانطَلَقَا حَتَّىٰٓ إِذَا لَقِيَا غُلَٰمًا فَقَتَلَهُۥ قَالَ أَقَتَلْتَ نَفْسًا زَكِيَّةًۢ بِغَيْرِ نَفْسٍ لَّقَدْ جِئْتَ شَيْـًٔا نُّكْرًا ﴿٧٤﴾

[18:74] Sai suka tafi. Da suka hadu da yaro qarami, sai ya kashe shi. Ya ce, "Don me ka kashe irin wannan mutum mara laifi? Lalle, ka aikata qazamin aiki."

۞ قَالَ أَلَمْ أَقُل لَّكَ إِنَّكَ لَن تَسْتَطِيعَ مَعِىَ صَبْرًا ﴿٧٥﴾

[18:75] Ya ce, "Ashe ban gaya maka ba cewa ba za ka iya juriya tare da ni ba?"

قَالَ إِن سَأَلْتُكَ عَن شَىْءٍۭ بَعْدَهَا فَلَا تُصَٰحِبْنِى ۖ قَدْ بَلَغْتَ مِن لَّدُنِّى عُذْرًا ﴿٧٦﴾

[18:76] Ya ce, "Idan na sake tambayar ka wani abu kuma, to, kada ka bar ni tare da kai. Ka ga yawan uzuri daga gare ni."

فَانطَلَقَا حَتَّىٰٓ إِذَآ أَتَيَآ أَهْلَ قَرْيَةٍ ٱسْتَطْعَمَآ أَهْلَهَا فَأَبَوْا۟ أَن يُضَيِّفُوهُمَا فَوَجَدَا فِيهَا جِدَارًا يُرِيدُ أَن يَنقَضَّ فَأَقَامَهُۥ ۖ قَالَ لَوْ شِئْتَ لَتَّخَذْتَ عَلَيْهِ أَجْرًا ﴿٧٧﴾

[18:77] Sai suka tafi. Har da suka kai ga mutanen wata alqarya, suka nemi mtanenta da su basu abinci, sai suka qi su yi masu liyafa. Jim kadan, sai suka ga wani bango a cikinta ta kusan ta fadi, sai ya gyara ta. Ya ce, "Ai da ka nemi su biya ka ujiri a kansa!"

قَالَ هَٰذَا فِرَاقُ بَيْنِي وَبَيْنِكَ ۚ سَأُنَبِّئُكَ بِتَأْوِيلِ مَا لَمْ تَسْتَطِع عَّلَيْهِ
صَبْرًا ﴿٧٨﴾

*Kome Yana da Dalilinsa.*

[18:78] Ya ce, "Yanzu ya wajabta mu rabu. Amma zan byyana maka kome da baka iya yin juriya ba a kansa.

أَمَّا ٱلسَّفِينَةُ فَكَانَتْ لِمَسَٰكِينَ يَعْمَلُونَ فِي ٱلْبَحْرِ فَأَرَدتُّ أَنْ أَعِيبَهَا
وَكَانَ وَرَآءَهُم مَّلِكٌ يَأْخُذُ كُلَّ سَفِينَةٍ غَصْبًا ﴿٧٩﴾

[18:79] Amma bisa ga girgin, ta kasance na wadansu matalauta ne masu kamun kifi, kuma na so in aibanta ta. Saboda akwai wani sarki a gaba zuwa gare su, wanda yana qwatar kowane girgi, da qarfi.

وَأَمَّا ٱلْغُلَٰمُ فَكَانَ أَبَوَاهُ مُؤْمِنَيْنِ فَخَشِينَآ أَن يُرْهِقَهُمَا طُغْيَٰنًا
وَكُفْرًا ﴿٨٠﴾

[18:80] "Kuma yaron, iyayensa muminai ne na qwarai, kuma mun ga cewa zai kallafa masu da bijirewa da kafirci.*

**18:80 Adolf Hitler da can kyakkyawa ne kuma ana ganin shi mara laifi. Da ya mutu yana yaro, da mutane masu yawa sun yi baqin ciki, kuma da wasu masu yawa ma sun jahilci hikimar Allah. An sanar da mu daga wadannan darussa da cewa kome da ya faru yana da dalilinsa*

فَأَرَدْنَآ أَن يُبْدِلَهُمَا رَبُّهُمَا خَيْرًا مِّنْهُ زَكَوٰةً وَأَقْرَبَ رُحْمًا ﴿٨١﴾

[18:81] “Sai muka yi nufin cewa Ubangijinsu, Ya musanya masu wani da mafi alheri da shi; wanda ya fi kirki da tausayi.

وَأَمَّا ٱلْجِدَارُ فَكَانَ لِغُلَٰمَيْنِ يَتِيمَيْنِ فِى ٱلْمَدِينَةِ وَكَانَ تَحْتَهُۥ كَنزٌ
لَّهُمَا وَكَانَ أَبُوهُمَا صَٰلِحًا فَأَرَادَ رَبُّكَ أَن يَبْلُغَآ أَشُدَّهُمَا
وَيَسْتَخْرِجَا كَنزَهُمَا رَحْمَةً مِّن رَّبِّكَ ۚ وَمَا فَعَلْتُهُۥ عَنْ أَمْرِى ۚ ذَٰلِكَ
تَأْوِيلُ مَا لَمْ تَسْطِع عَّلَيْهِ صَبْرًا ﴿٨٢﴾

[18:82] Amma dangane da banon, ya kasance na wadansu yara biyu ne, marayu a cikin birnin. Qarqashinta, akwai dukiya wanda na su ne. kuma babansu ya kasance salihin mutum ne, saboda haka Ubangijinka Ya nufe su, su yi girma kuma su kai ga iyakn qarfinsu, sa’annan, su cire dukiyarsu. Saboda wannan rahamah ne daga Ubangijinka. Ban aikata kowanensu bisa son ra’ayin kaina ba. To, bayanin abin da baka iya ka haqura a kansa ba kenan.”

وَيَسْـَٔلُونَكَ عَن ذِى ٱلْقَرْنَيْنِ ۖ قُلْ سَأَتْلُوا۟ عَلَيْكُم مِّنْهُ
ذِكْرًا ﴿٨٣﴾

*Wani Mai Qaho Biyu Ko Kuma Mai Zamani Biyu*

[18:83] Kuma suna tambayar ka game da Zul-Qarnain. Ka ce, “Zan karanta maku wasu labarunsa.”

إِنَّا مَكَّنَّا لَهُۥ فِى ٱلْأَرْضِ وَءَاتَيْنَٰهُ مِن كُلِّ شَىْءٍ سَبَبًا ﴿٨٤﴾

[18:84] Lalle ne, Mun ba shi mulki a cikin qasa, kuma muka ba shi hanyoyin abubuwa dabam dabam.

فَأَتْبَعَ سَبَبًا ﴿٨٥﴾

[18:85] Sa’annan, ya bi hanya guda.

حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ مَغْرِبَ ٱلشَّمْسِ وَجَدَهَا تَغْرُبُ فِى عَيْنٍ حَمِئَةٍ وَوَجَدَ عِندَهَا
قَوْمًا ۗ قُلْنَا يَٰذَا ٱلْقَرْنَيْنِ إِمَّآ أَن تُعَذِّبَ وَإِمَّآ أَن تَتَّخِذَ فِيهِمْ حُسْنًا ﴿٨٦﴾

[18:86] Sa’ad da ya kai nesa da yamma, sai ya ga rana na fadiwa a cikin qaton teku, kuma ya sami mutane daga wurin. Muka ce, “Ya Zul-Qqrnain, (ka yi mulki yadda kake so); imma za ka azabtar, ko ka kyautata zuwa gare su.”

قَالَ أَمَّا مَن ظَلَمَ فَسَوْفَ نُعَذِّبُهُۥ ثُمَّ يُرَدُّ إِلَىٰ رَبِّهِۦ فَيُعَذِّبُهُۥ عَذَابًا نُّكْرًا ﴿٨٧﴾

[18:87] Ya ce, “Bisa ga wadanda suke zalunci, za mu azabta su, sa’annan, idan suka koma ga Ubangijinsu, sai kuma Ya qara masu azaba mai muni.

وَأَمَّا مَنْ ءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحًا فَلَهُۥ جَزَآءً ٱلْحُسْنَىٰ ۖ وَسَنَقُولُ لَهُۥ مِنْ أَمْرِنَا
يُسْرًا ﴿٨٨﴾

[18:88] “Amma ga wadanda suka yi imani kuma suka aikata ayyuka na qwarai, suna samun kyakkyawan lada; za mu kyautata masu.”

ثُمَّ أَتْبَعَ سَبَبًا ﴿٨٩﴾

[18:89] Sa’annan kuma ya bi wani hanya.

حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ مَطْلِعَ ٱلشَّمْسِ وَجَدَهَا تَطْلُعُ عَلَىٰ قَوْمٍ لَّمْ نَجْعَل لَّهُم مِّن
دُونِهَا سِتْرًا ﴿٩٠﴾

[18:90] Sa’ad da ya kai nesa da gabas, ya ga inda rana ke fitowa a kan mutane wanda ba su da abin da za su tsare kansu daga ita.

كَذَٰلِكَ وَقَدْ أَحَطْنَا بِمَا لَدَيْهِ خُبْرًا ﴿٩١﴾

[18:91] Tun asali, mu ne mafi sani ga kome da ya gani.

ثُمَّ أَتْبَعَ سَبَبًا ﴿٩٢﴾

[18:92] Sa’annan ya bi wani hanya.

حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ بَيْنَ ٱلسَّدَّيْنِ وَجَدَ مِن دُونِهِمَا قَوْمًا لَّا يَكَادُونَ يَفْقَهُونَ
قَوْلًا ﴿٩٣﴾

[18:93] Sa’ad da ya kai ga kwari tsakanin kawarai, sai ya tarad da mutanen da daqyar ake fahimtar yarensu.

قَالُوا۟ يَٰذَا ٱلْقَرْنَيْنِ إِنَّ يَأْجُوجَ وَمَأْجُوجَ مُفْسِدُونَ فِى ٱلْأَرْضِ فَهَلْ نَجْعَلُ لَكَ
خَرْجًا عَلَىٰٓ أَن تَجْعَلَ بَيْنَنَا وَبَيْنَهُمْ سَدًّا ﴿٩٤﴾

*Ya’juj Da Ma’juj**

[18:94] Suka ce, “Ya Zul-Qarnain, lalle ne, Ya’juj da Ma’juj masu barna ne a cikin qasa. To, ko mu biya ka domin ka sanya shingen danni tsakaninmu da su?”

**18:94-98 Daya daga cikin ayyukan manzon Allah na Wa’adi shi ne ya ayyane cewa Ya’ajuja da Ma’ajuja, alamar qarshe kafin qarshen duniya, za su sake fitowa cikin shekara 2270 AD (1700 AH), ya rage shekaru 10 kawai kafin qarshe. A lura cewa Ya’ajuja da Ma’ajuja sun auku a cikin Surah 18 da 21, watau ayoyi 17 daidai kafin qarshen kowane surah, a madadin shekarun qirgan watan Muhammadiya (dubi 72:27 da shafi 25).*

قَالَ مَا مَكَّنِّي فِيهِ رَبِّي خَيْرٌ فَأَعِينُونِي بِقُوَّةٍ أَجْعَلْ بَيْنَكُمْ وَبَيْنَهُمْ رَدْمًا ﴿٩٥﴾

[18:95] Ya ce, "Ubangijina Ya mallaka mini karimci mai yawa. Idan kuka bani hadin kai, zan gina datsiya tsakaninku da su.

ءَاتُونِي زُبَرَ الْحَدِيدِ حَتَّىٰ إِذَا سَاوَىٰ بَيْنَ الصَّدَفَيْنِ قَالَ انفُخُوا حَتَّىٰ إِذَا جَعَلَهُ نَارًا قَالَ ءَاتُونِي أُفْرِغْ عَلَيْهِ قِطْرًا ﴿٩٦﴾

[18:96] "Ku kawo mini qarafuna masu yawa." Sa'alin da ya cike gurbin tsakanin kawaran biyu, ya ce, "Ku hura." Da ya yi jan zafi, ya ce, "Ku taya ni kwarara kwalta a kansa."

فَمَا اسْطَاعُوا أَن يَظْهَرُوهُ وَمَا اسْتَطَاعُوا لَهُ نَقْبًا ﴿٩٧﴾

[18:97] Ta haka ne, ba za su iya hawanta ba, kuma ba za su iya huda ramuka a cikinta ba.

قَالَ هَٰذَا رَحْمَةٌ مِّن رَّبِّي فَإِذَا جَاءَ وَعْدُ رَبِّي جَعَلَهُ دَكَّاءَ وَكَانَ وَعْدُ رَبِّي حَقًّا ﴿٩٨﴾

[18:98] Ya ce, "Wannan wata rahamah ce daga Ubangijina. Sai idan wa'adin Ubangijina ya zo, zai sa datsiyan ta marmashe. Kuma wa'adin Ubangijina gaskiya ne."

۞ وَتَرَكْنَا بَعْضَهُمْ يَوْمَئِذٍ يَمُوجُ فِي بَعْضٍ وَنُفِخَ فِي الصُّورِ فَجَمَعْنَاهُمْ جَمْعًا ﴿٩٩﴾

[18:99] A lokacin ne, za mu bari su yi shigan farmakin juna, sa'anna a busa qaho, kuma mu tara su duka gaba daya.

وَعَرَضْنَا جَهَنَّمَ يَوْمَئِذٍ لِّلْكَافِرِينَ عَرْضًا ﴿١٠٠﴾

[18:100] Kuma mu gabatar da Jahannama, a ranar, ga kafirai gittawa.

ٱلَّذِينَ كَانَتۡ أَعۡيُنُهُمۡ فِي غِطَآءٍ عَن ذِكۡرِي وَكَانُواْ لَا يَسۡتَطِيعُونَ سَمۡعًا ١٠١

[18:101] Wadanda idanunsu suka kasance a rufe da tunawa da Ni. Kuma sun kasance ba su iya saurarawa ba.

أَفَحَسِبَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَن يَتَّخِذُواْ عِبَادِي مِن دُونِيٓ أَوۡلِيَآءَۚ إِنَّآ أَعۡتَدۡنَا
جَهَنَّمَ لِلۡكَٰفِرِينَ نُزُلٗا ١٠٢

[18:102] Shin, wadanda suka kafirta suna zoton za su tsira ne da sanya bayiNa majibinta baici Na? lalle, mun shirya Jahannama ta zama liyafa ga kafirai wurin zama na dindin.

قُلۡ هَلۡ نُنَبِّئُكُم بِٱلۡأَخۡسَرِينَ أَعۡمَٰلًا ١٠٣

*Ka Binciki Kanka*

[18:103] Ka ce, Ko in gaya maku game da mafifita hasara ga ayyuka?"

ٱلَّذِينَ ضَلَّ سَعۡيُهُمۡ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَهُمۡ يَحۡسَبُونَ أَنَّهُمۡ يُحۡسِنُونَ صُنۡعًا ١٠٤

[18:104] Su ne wadanda ayyukansu a cikin wannan rayuwar duniya suke kan bata, amma suna zaton suna kyautata ayyukan qwarai."

أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمۡ وَلِقَآئِهِۦ فَحَبِطَتۡ أَعۡمَٰلُهُمۡ فَلَا نُقِيمُ لَهُمۡ
يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَزۡنٗا ١٠٥

[18:105] Wadannan su ne suka kafirta da ayoyin Ubangijinsu kuma da haduwa da Shi. Saboda haka, ayyukansu duk abanza ne; kuma a Ranar Alqiyamah, awonsu ba za su yi nauyi ba.

ذَٰلِكَ جَزَآؤُهُمْ جَهَنَّمُ بِمَا كَفَرُوا۟ وَٱتَّخَذُوٓا۟ ءَايَٰتِى وَرُسُلِى هُزُوًا ١٠٦

[18:106] Sakamakonsu shi ne Jahannama, saboda kafircinsu, kuma saboda sun mayar da ayoyiNa da manzanniNa abin yin ba’a.

إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ كَانَتْ لَهُمْ جَنَّٰتُ ٱلْفِرْدَوْسِ نُزُلًا ١٠٧

[18:107] Amma ga wadanda suka yi imani kuma suka aikata ayyuka na qwarai, to, sun cancanci Aljannar Firdausi ta zama liyafa a gare su.

خَٰلِدِينَ فِيهَا لَا يَبْغُونَ عَنْهَا حِوَلًا ١٠٨

[18:108] Suna madauwama a cikinta; ba za su bukaci wani musayanta ba.

قُل لَّوْ كَانَ ٱلْبَحْرُ مِدَادًا لِّكَلِمَٰتِ رَبِّى لَنَفِدَ ٱلْبَحْرُ قَبْلَ أَن تَنفَدَ كَلِمَٰتُ رَبِّى وَلَوْ
جِئْنَا بِمِثْلِهِۦ مَدَدًا ١٠٩

*Alqur’an: Kome Ne Da Muke Bukata*

[18:109] Ka ce, “Idan da ruwan teku tawada ce ga (abin rubutun) kalmomin Ubangijina, da tekun ta qare, kalmomin Ubangijina basu qare ba, kuma ko da mun ninka misalin tawadar ne.”

قُلْ إِنَّمَآ أَنَا۠ بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ يُوحَىٰٓ إِلَىَّ أَنَّمَآ إِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَٰحِدٌ ۖ فَمَن كَانَ يَرْجُوا۟ لِقَآءَ
رَبِّهِۦ فَلْيَعْمَلْ عَمَلًا صَٰلِحًا وَلَا يُشْرِكْ بِعِبَادَةِ رَبِّهِۦٓ أَحَدًۢا ١١٠

[18:110] Ka ce, “Ni mutum ne kawai kamarku, ana yin wahayi zuwa gare ni cewa: Abin bautawarku Daya ne. Saboda haka, wadanda suke fatan su hadu da Ubangijinsu, to sai su aikata ayyuka na qwarai, kuma kada su hada kowa ga bauta ga UbangijinSa.”